alamun tanƙwara ,abun da yace yayi masa kawai shine ,babu wanda ya isa ya hana shi , sai idan yaso". Shiru Adda Raliya tayi idon ta na kaɗawa , wannan wacce irin rayuwa ce Ammie ta jefa Habab? Taasa masa tsanar mahaifiyar sa ,baya marmari n ta irin na uwa da ɗa, anya Ammie abun da take tana kyautawa kuwa??". Duk Adda Raliya ke maganan a zuciyar ta ,kamin taji Muryar Zainabu ya katseta tana cewa " Adda Raliya na shirya mu tafi ko??? . Miƙewa Adda Raliya tayi jiki a sanyaye ba ƙwari suka nufi side ɗin Hajiya Luba". A falon suka tadda su kaman yanda suka bar su , sai dai a wannan karon ba Habab ba Sobreen. Zama Zainabu tayi tana gaishe dasu Hajiya Luba da Shema ,wanda dukan su a fuska sake suka amsa mata tamkar ba wani abu a tare dasu....Mmkin wannan sauyin Zainabu keyi kana ta tsinkayi muryar Hajiya Luba tana cewa " Zainab hau sama ki kira Habab da Sobreen ,su sauko haka nan".

Miƙewa Zainabu tayi a hankali su duka suna bin ta da kallo, a zuciyar su suna cewa " Shegiya ƴar matsiyata ta samu wuri ai dole ta buɗe ba abun da ya dameta, wato mu ta barmu ga ƴan iska , zaki san waye Hajiya Luba". Ita dai Zainabu dake juya jiki tamkar ɗawisu don ita kanta tana ɗan jin yanda jikin nata yayi mata nauyi. A hankali ta haye stairs ɗin falon tana nufan up don ta shaida masu kirar Hajiya Luba".

Wani irin dammm yaji ƙirjin ta ya buga mata , gani tayi Habab ƙawance a 3strr na falon da ya ƙawatu matuka , gyefe Sobreen ce zaune tana kissing ɗin bakin shi..... Shima yana nata , ji tayi tamkar ta juya ,amma kuma babu yanda ta iya , Cikin zazzaƙar Muryar ta tayi masu sallama, wanda babu wanda ya amsa mata , sai dai dakatawa da sukayi da yin komai ". Hajiya ce tace nayi kirar ku ƙasa". Kauda kai Sobreen tayi sai Habab ne yace " Okay! Ficewa tayi daga falon tana sauka don faɗa mawa Hajiya Luba , nan taga babu kowa a falon sai Adda Raliya.... Zama tayi gyefen Hjy Raliya tana cewa " Adda Raliya ina Ammie??. Tana ɓangaren Daddy jeki dubata can . Ita dai ji tayi kaman an cire mata laka , a haka ta nufi ɓangaren Alh Ahmadu , a falo ta tadda Shi da Hjy Luba ,wanda ganin haka yasa ta zubewa saman carpet ,kamin tayi magana yana murmushi don ita har mmkin fara'ar shi take , duka ƴaƴan shi babu wanda yayo sa. Mutanen Japan Zainab ɗiyata kinga dai gari ko? Bai rufe ki a gida ba don Nasan halin Habab sarai". Dariya Zainabu tasa har da ƙyaƙyatawa , kaman ba sirikin ta ba ta matsa kusa dashi tana cewa " Eiyee Daddy munje wallahi ƙasar tana da kyau gaskiya". Nan Zainabu ta hau Bama Daddy labrn japaan da yanda Suka yawuta da Habab. Fira sosai suke da Daddy har sun manta da Hajiya Luba dake zaune tamkar wacce aka dasata ji take tamkar ta kashe ɗayan cikin su ta huta.
Miƙewa tayi ne zata fita don baƙin ciki ya nata sukuni har ɗigar zufa take yi . Muryar Zainabu taji tana cewa " Daddy aiko na faɗa maka munga Mahaifiyar Habab a Japan!

Wani irin jiri ne ya ɗibeta , wanda yasata saurin dage bango tana shirin faɗi taimakon ta bangon da ta riƙe. Saurin aje jaridar hannun shi yayi yana kallon Zainabu jikin sa har rawa yake yana cewa " Zainab a ina kike ga Salma?? Ina take tare kuka zo?? A'a Daddy , Habab yaki.... inalillahi wa'inna ilaihir raji'un wannan wani irin yaro ne??? Bai taho mun da  Salma ba ?? Daga can yasan inda zata tafi ! Ƙoƙarin miƙewa yakeyi yana dafe ƙirjin shi da yakejin tayi masa nauyi

yana fara tari.....Saurin matsawa gareshi sukayi cikin sauri , wanda kamin ta isa Hjy Luba ta dafe shi tana zaunar dashi ,cikin wani irin murya mai kama da kuɗu tace " Zainab maza jeki falo ki ɗauko mun ruwa na basa.....Ruɗu da firgicin yasa Zainabu sam ta manta da wani fridge ,wannan yasata nufar falo da sauri don ta ɗauko ruwar".

Minti biyu ta dawo da ruwa a hannun ta , wanda hango Daddy tayi a kujerar babu alamun rai a tare dashi , kumfa mai kaman jini na fita ta bakin shi, sam ba Hajiya Luba a wurin....sakin ruwan tayi tsana nufan sa da sauri tana riƙo hannun da kirar sunan shi " Daddy ga Ruwan , daddyyyy!!

A bayan ta ne taji ihun Shema'u tana faɗin " Inalillahi wa'inna ilaihir raji'un mun shiga uku ta kashe mana uba , Kuzo Safiya Adda Raliya shiknnn Zainabu ta kashe Daddy!!! ,Wani irin bugawa ƙirjin Zainabu yayi , wanda kamin kice kobo duka sukayo falon har da Habab da Sobreen da suka nufo inda Zainabu da Har a lokacin take riƙe da hannun Daddy". Girgiza Alh Ahmadu Habab keyi yana kirar sunan sa ,Sobreen ko ta ɗaura hannu aka tana tsala ihu....dai dai Hajiya Luba na sakkowa da gudu hannayen ta asaman kanta....kallon Zainabu tayi kamin tace " Zainabu me mukayi maki?? Me mukayi maki kike Son rusa duk wani farin cikin mu..mijina zaki kashe waye ke??? Habab ka ɗauko mana guba , kinyi yunƙurin kashe Habab bai yiwu maki ba shine zaki kashe mahaifin sa , kika sa da yaudara ??? Hawaye ne ya hau bin kuncin Zainabu sharrrr ³ ba ƙaƙƙautawa , buɗe baki tayi da ƙyar kanta yayi mata nauyi ,Hajiya wallahi bani ba....ji tayi tassss² Safiya tana wanke fuskar ta da wani irin gigitaccen mari, wanda yasa maganan nata ta ɗauke.....Baƙa mai baƙar aniya shiknnn lahaula walahhh Zainab me mukayi maki a rayuwa? Wayyo Daddy !!!! Safiya tayi maganan tana baya rigijajaaaa wai adole ta sume ..... Shema ne da Hajiya Luba suka hau ihu suna riƙe ta shiknnn za'ayi biyu......

Zee me Daddy yayi maki zaki kashe shi? Ta tsinkayi muryar Habab da yake takowa inda take kamar kumurci , a wannan lokaci n duk tsoran sa ta fice mata,tsayawa tayi ji take kawai ya kasheta itama ta huta da wannan rayuwar! Ka yarda kai ma Ni Zainabu xan iya kisa?? Kisan na wai na kashe Daddy??. Wani mari ya ɗauketa dashi da sai da cikin ta ya murɗa mata tana ganin tartsatsin wuta..... Tun da kika ce kina Son na , Nasan da wata abun da kke kulawa , sai ki nemi kashe mun Mahaifi?? Wani marin ya ɗauke ta dashi da sai da ta kira ,bakin ta na fashewa da jini ,fuskar ta shatin hannayen sun fito raɗa raɗa". Gaban sa Adda Raliya tayo tana cewa " Habab ka natsu tayaya Zainabu zata kashe Daddy??? .

Adda Raliya Daddy ne fa, sai kace ba mahaifin ki ba , to waye zai kashe shi anan gidan...kuma sawa aka same shi??? Shema'u tayi maganan cikin Muryar matsanancin kukan karya.....wanda jin haka n yasa Adda Raliya fashewa da kuka ,ita dai tana jin kokonto a zuciyar ta ,amma kuma waye zai kashe masu mahaifi?? ....yanda kika kashe mun Mahaifi wallahi kema yau sai na sa bindiga na harbeki ,ko na kasheki da duka. Habab yayi maganan fuskar da duk ta sauya ya koma Habab ɗin ɗan da a lokacin suma kansu tsoran sa sukeji ,don sun san zai iya komai.

A wannan karon sam Zainabu takasa kukan sai hawaye....Ina ai mu kira jami'ai su fita da ita...daga baya ayi bayani n komai ,Cewan Hajiya Luba tana goge hawayen fuskar ta".

Ina ne xa'a tafi da Zainab ɗin ?? Sukaji wata Muryar da basu san ta wacece ba ya katse su daga bayan su". Cikin sauri su duka suka waigawa don ganin wacece ke faɗin wannan magana". Wani irin razana Hajiya Luba tayi kana cikin wata irin murya ta ce " Salma??".

Bata amsa ta ba sai cewa tayi " Ina a raye Sirikata matar Habab wai a yari? Abun da kikeso kenan ,to koda komai nawa da na mallaka xai ƙare sai dai ya ƙare ,baxan taɓa barin hakan ta faru ba. Aiko wallh ba'a isa ba ,ta kashe mana Daddy kice ba za'a ɗau mataki ba, dama ƙila ke kika saka ta! Shema ke maganan cike da ƙunar rai...ji take kaman ta haɗa su su duka ta kashe . Tsayawa Habab yayi cakkk yana kallon Zainabu da lokaci ɗaya kamanin ta sun sauya saboda marin da suka dingi zagba mata , jin tsanar ta yake a kowani sekan , Jinin yaga yana bin ƙafarta , wanda kamin yayi magana ne yaji Muryar Momy tana cewa" Ai mahaifin naku bai mutu ba , da kanshi xaiyi bayani in Zainabu ce take yunƙurin kashe shin zai faɗa.

DPO taji tayi kirar DPO wanda cikin gaggawa suka shigo da mutanen sa , kuɗauki Alh Ahmad akai shi asibiti mafi sauri kuma mai tsaro sosai....Ni xan tafi da Zainab ...Habab wallahi sai kayi nadama ,ko nace tun daga yau zaka fara nadama , Zee ce xata iya aikata wannan abun ,har kake marin ta , saboda tana ƙaunar ka a rayuwa , to Ni daga yau na rabaku da Zainab har abada babu kai babu ita....kaje kayi rayuwar ka da matar da kake so mai son ka da gaskiya.

Tana faɗin haka tana takowa inda zainabu ke riƙe da marar ta da taji yana wani irin juya mata, numfashi ta sauke da ƙarfi ,wanda ya maido hankula n su Hjy Luba nan suka ga jini na bin ƙafarta ,alamun ɓari tana da ciki yana shirin fita ko ma ya fita.....baya tayi luuuuuu idon ta na rufewa ,wanda yasa Mom Salma saurin riƙe ta ,tana ƙara kirar police da sauri Hjy Raliya ta kama Zainabu suna ficewa da ita daga falon haɗi da nufar farfajiyar gidan ,wanda Tuni aka nufi da Daddy asibiti don ceto rayuwar sa..................

*Babban sirrin qamshi kisamu hadadden gaske Wanda y Sami qwararriyr me sarrafashi daga very expressive product like arabian,rasasee ajmal,and alharamaiin.masu asalin kyau d inganci er'uwa karkiyi sake d attitude naki qamshi shine ke bayyana ke wacece ko kinyi ado ko bakiyiba. Mummies kujini dakyau the beauty of turare is speak to ur hearts and hoply to someone else...namiji na iya manta komi amma Banda special qamshin ki daya Saba jii na yauda gobe farkon matakin Jan hankalin miji gareki shine y shaki qamshin daddadan turarenki.🥰💃💯 Akwai wasu sirruka ajikin qamshi turaren da akeyinsa da wasu daga cikin

itatuwan bishiyoyi ko saiwar wasu bishiyoyi Wanda ake Kira da (eriqh) wannan itatuwa ba kowa ya iya maintaining dinsu subada abinda ake bukataba da wannan zakuga d yawan masu turaren wuta insunyi turare yake qauri Wanda dazasu dage su sarrafashi yanda y kamata Ina me tabbatr muku ba boka ba malam kinadaga cikin gidanki Zaki siye zuciyr oga walhi kusamu lada hankali kwance💃💃💯 Wanda mu haka shine birinmu insha Allah. To ku marmatso kusa kuji shahararriyar Kuma hamshakiyr mesai da turarukan wuta wato UMSAD INCENSE ta tanadar muku turaruka masu inganci Kama daga jiki,gida,Kaya, turarukan tsuguno, turarukan daake shafawa a gashi batare da sunbawa gashi matsala ba ds.kudai kawai ku tuntube ta 08028827241 /09033791049 karku manta UMSAD INCENSE jindadinku shine namu 💯💃💃

*Littafin ƙwrtn mny na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne  MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932 "Tncuuu".🤝🏻*

*Mmn teddy🧸*
[6/30, 14:39] my number: *🕊️KWRTN MANYA🕊️*

_*Mmn teddy*_
32

*Littafin na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932🤝🏻*

Mutane da yawa na tambaya na littafai na , akan wai na basu ko a tunanin su free books ne ban dai sani masu ba , Ni abun ma sometimes dariya yake bani wallahi🤣🤣 wai sai kawai kizo mun na baki code ɗin littafin ,nace maku na kuɗi ne , wasu ƴan anacen sai su rinƙa cewa " Ai suna dashi password ɗin kawai xan faɗa masu😹😹 to ke kika rubuta littafin ko Ni?? Haba don Allah , maganan gaskiya littafan Mmn teddy na kuɗi ne duka kaman su:
Ƴar aikina
Ƴar waye
Dijama ƴar Fulani
Bafullatanan Ruga
Siyasata
Kawaliya
Walijaam
Gidan ƙwarata
Habibi da'iman
Bintoto

Gidan zaurawa
Da dai sauran su ,Gamai buƙatar samun su ,zai iya mun mgn ta private . Gasunan dai da wanda ma ban faɗo su ba, duk dai na kuɗi ne plz...

******

Haka Hajiya Salma da Adda Raliya suka nufi asibiti da Zainabu cikin gaggawa. Tuni akayi emargency da ita ,wanda kamin ƴan mintuna tuni likitoci suka rufa mata , kowa na ƙoƙarin ganin sun ceto rayuwar ta....don a halin da take ciki komai ka iya faruwa da ita". Kai komo Dr Salma keyi kamin ta buƙaci ruwa don tayi alwala takai kukan ta ga Allah , yayi masu maganin duk wata damuwa".

Ɓangaren Alh Ahmadu kuwa duba da ƙwararrun likitocin da suka rufa masa ne yasa nan da nan suka shawo kan matsalar tasa ,tuni suka samu dai dai ruwar numfashin sa ,sai dai Oxcygen da aka saka masa sakamakon Guba da Hajiya Luba ta basa , wannan yasa numfashi n sa da ƙyar suka samu daidaituwar komai". Habab bai dawo hankalin shi ba sai da aka ce masa mahaifin sa ya farfaɗo kuma zai iya cigaba da rayuwa inshaallh". Wannan yasa shi sauke ajiyar zuciya yana hamdala ga Allah . Abun da ya ɗaure masa kai shine tun da suka isa asibitin ba Hajiya Luba ba labarin ta , haka ma ba Sobreen , Shema'u ce da Safiya ,wanda suna suna jin ance Zai iya cigaba da rayuwa nan suka silale suna guduwa daga Asibitin.

*****

Inalillahi wa'inna ilaihir raji'un ,shikenan Ammie wallahi kin cuce mu! Yanxu ya zamu yi ,gashi kinyi yunƙurin kashe san ,amma bai mutu ba , kar mu tashi ba tsuntsu ba tarko mana , mu bamu ci dukiyar mahaifin namu ba ,kuma bamu ci na Habab ɗin ba ,Shema tayi maganan cike da hasala . Jikin Hajiya Luba tuni yayi sanyi ta rasa ta ina zata fara ,tabbas tasan ƙarshen duk wani sharrin ta ne ya zo". Sobreen ne cike da kuka tace " Ammie me yasa to baki haɗa su su duka kin basu guban ba? , Kalli fah Zainabu har cikin Habab take ɗauke dashi , yanxu ya zamu yi Daddy ya rufa asiri komai kar ya tona???. Cewan Sobreen tana juyawa ga Hajiya Luba dake girgiza kai cike da jin ɗaci tace " Ban taɓa sa hannu a abu ba'ayi nasara ba , amma shigowa r wannan yarinyar ta ruguxani ta lalatani, wallahi bazai sabu ba , dole cikin ɗaya za'ayi ɗaya.....Dole Nasan duk yanda xanyi Alh Ahmadu ya mutu a yau ,ko da nawa ne xan biya don ganin hakan ya faru".

Habab ne ya shigo falon fuskar shi a haɗe wani irin gumi ke karyo masa , mamaki ne ya kama sa , ganin sa yasa su duka miƙewa kowa tana rarraba ido na mare gaskiya". Ammie da gaske kece kike ƙoƙarin kashe Ni da Daddy? Wai ba mafarki nakeyi ba ,Ammie kece dai?? Yayi Magana n cikin wata irin murya ,kansa na sara masa ji yake tamkar zai fashe.......shigowa Hjy Raliya tayi tana goge hawayen idon ta kana ta dafa Habab tana cewa " Kayi kuskure Habab daka yarda da Ammie , Ammie bazata taɓa Sonka ba , tun da ba ita ta haifeka ba, kuma bata ƙaunar Mom Salma". Ka koma ka ba Momy haƙuri akan abun da kayi mata , haka yarinyar

mutane da bataji ta gani ba , kayi mata wannan tijara".

Ke Raliya zan tsine maki ,yanxu da maƙiyana ne kika haɗa kai Raliya? Wallahi yau ina baki wasa ba zan tsine maki ". Tsinuwar ki bazata taɓa kama ta ba Luba!! Suka ji Muryar Daddy ya katse su da basu san ta ina yazo ba.....a keken marasa lafiya a ka ƙariko dashi tsakiyar falon. Hajiya Luba na riƙe ki tsakani da Allah ,ashe dama tuni don wani abu nawa kike zaune dani ,kina jirar wata dama ce , sai yau kika samu kika aikata ,kuma saboda zalunci ki kika laƙaba mawa yarinya bataji bata gani ba. Kije Hajiya Luba bana son ganin ki dake da duk wa'annan yaran naki , sunemi uba ba Ni ba , Kallon DPO Bashir yayi kana yace " Ku tasa su subar mun gida na ,bance gomnati tayi masu komai ba ,amma Allah zai masu don zasu ga sakayya inshaallh".

Kasa motsawa Habab yayi kaman an Dass shi ,wasu irin ƙwallah ne kebin kuncin sa ,wanda rabon da yaji su ya manta a rayuwa . Haka Cike da ihu aka tasa Hajiya Luba da gayyar ta suna ficewa daga gidan Alh Ahmadu , kaman wasu korarru.... Kamin su fice ne Ɗahatatu da taji labarin komai tuni ta shirya kayanta tana bin hanyar ƙauyen garin su".

Haka ma'aikatan gidan kebin Hjy Luba da ƴaƴan ta da Allah tsine ,da jin haushin su akan abun da suka aikata ,ana masu alawadai....kamin kace kobo gaba ɗaya Lagos ta ɗauka kan abun da mata sukayi mawa wannan shahararren Attajiri wato Alh. Ahmadu Billionerer. Kowa da abun da yake cewa " kafofin sadarwa ba abun dake kai kawo sai hotunan Hjy Luba da faɗin abun da ta aikata mawa mijin ta da ƴaƴan ta , har maganan Dr Salma sai da ya shigo kowa na binsu da ala wadai.....

Tsawon kwana biyu Habab ya kasa fita ko nan da can , kullum yana ɓangaren shi abun duniya ya ishe shi....Saif yazo shida Sadeeq ba adadi amma ina ,ba halin da suke ganin shi sai a na shan barasa da busa sigari kullum yana cikin wannan yanayi . Bashi da aiki sai na tunanin wani hali Zainabu ke ciki? Duk da Adda Raliya ta shaida masa da tana lafiya sai dai tayi miss carriage... So yake yaje yaga su amma kuma bai san wani magana zai faɗo bakin su su duka ba , don yasan tabbas a yanxu ko so hauka ne Zainabu sai tayi fushi dashi , addu'a r da ma itace Allah yasa bata daina Son shi ba a zuciyar ta.

A ranan rahadi ne Adda Raliya ta tsare shi akan cewa " Ya yake ciki maganan auren sa da Sobreen ,bai bata amsa ba fache miƙewa da yayi yana nufar bedroom ɗin sa ,can sai gashi da takarda yana miƙawa Adda Raliya , na sake ta tun a ranan bana jin xan iya zama da ko wacce mace in dai ba Zainab ba". Ita kaɗai nake So Adda Raliya,ya xanyi ta dawo gareni ? Ina Son Zeee ina jin komai zai iya faruwa da Habab indai ya rasa ta a rayuwar shi . Rarrashin sa Adda Raliya ta hauyi , don ita kanta ta rasa tayaya zata shawo kan Mom Salma .

******

Yau Safiyar Laraba Tun safe Mom Salma ta haɗa mawa Zainabu komai kaman yanda ta saba , don gyara ta take sosai tana haɗa mata magunguna dana wanko dattin da duk yayi saura". Sosai Zainabu ta ɗan yi rama tayi haske na masu rashin lafiya....Rintse idon ta tayi tana zama a cushines ɗin falon tana tunanin ya xatayi ta cire Don Habab ta yaƙice ta huta a rayuwar ta! Mom Salma ce take jan ta da fira ganin duk ta chanja ,tamkar ba ita Zainabu n ba ,mai yawan surutu amma a yanxu sai tafi awa da awannin shiru ba uhm ba umh'uhm . Wannan yasa Momy ke ƙoƙarin jan ta ajiki da fira . Ƙamshin turaren sa ta ji tana shaƙar shi ,kana taji bugun ƙirjin ta ya daɗa ƙaruwa. Saurin miƙewa tayi tana kallon Hajiya Salma da itama ita ɗin take kallo. Momy Habab!! Miƙewa Momy tayi tana takowa inda take tsaye haɗi da kamata ,tana cewa " Waye Habab ki mance dashi a rayuwar ki Zeee , ki natsu ki rabu dashi zaki samu miji mai Sonki fiye da Habab , na bari ki warware ne sosai , ƙasar ma zaki bari kike kiyi karatun ki hankali ƙwance ". Momy ina ji ajikina kaman yana cikin gidan nan? Zainabu tayi magana hawaye na bin kuncin ta. Kamata Dr Salma tayi tana buɗe baki xatayi magana taji shigowar sa bakin sa ɗauke da sallama.

Dakewa Zainabu tayi itako Momy wani haɗe rai tayi , kaman batasan Habab ba a rayuwa. Wuce wa Zainabu tayi fuuuuuu tana yin ciki ba ko waiwaye ,wanda hakan sosai yayi mawa Mom Salma daɗi. Bata tanka shi ba ,har ya iso gabanta yana zama a ƙasa capet. Gaishe ta yafara ,wanda babu walwala take amsa masa...jin shirun sa ne yasa ta cewa " Lafiya wani abu ya kawo ka???.

Rintse idon sa yayi yana jin wani iri ,kana yace " Momy don ki yi hkr akan abun da ya faru , ki ba Zeee haƙuri ,na kasa sukuni rashin ta a tare dani , kice mata tazo tabi Ni mu koma gida!

Sakin baki Momy tayi tana kallon sa cike da mmkin rainin hankali irin na Habab, wanda cikin ɗaya murya ta kira sunan Zainabu .....wani irin sanyi yaji a zuciya r shi a tunanin shi Zainabu n ta kirata ne ta bashi kaman yanda yace ".

Zainabu ce ta fito fuskar ta a sake ,don tuni ta dake da komai. Momy !! Ta yi mgnn tana zuwa inda take ". Maimaita abun da kace ?? Tace ma Habab tana ware lulun idanun ta da ya ɗebo ta. Ɗago idon sa yayi da suka kaɗa cikin wani irin sanyi yace " Don Allah Zee ki taho mu koma gida ,na kasa jin daɗin rayuwa ta baki bazab iya zama ba tare dake ba a rayuwa ta , inaaaa". Eiyeee lallai malam , na rantse Habab bani babu kai ,baxan zauna dakai ba wallahi. Momy don Allah kar ki yarda da maganan da wallahi na koma kasheni zaiyi wallh".

Ai bari kuka Zainab ,babu inda zaki je ,to ko ita tace zata cika sai nace bata isa ba ,bare kai ƙaramin mutum ,kai Habab !! Babu ma inda zaka tafi sai ka rubuta mun takardar rabuwar ka da zeeee Baxan bari nasa ido ka cigaba da cutar musu da yarinya ba!!!!!

Wani irin bugawa ƙirjin Habab yayi wanda sai da yakai hannun shi yana dafe wurin ,don ji yake kaman zai ɓalle ya fito wajeeeeee!!!!

*Littafin ƙwrtn mny na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne  MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932 "Tncuuu".🤝*

Mmn teddy🧸
[7/1, 08:44] my number: *🕊️ƘWRTN MANYA🕊️*

_*Mmn teddy*_
33

*Littafin na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932🤝*

****

Ɗago da lulun idanun sa yayi da suka rine suka sauya daga fari zuwa jah". Ehh kaji abun da nace maka ko?? Cikin wani irin jiri da ƙyar ya iya cewa " Momy! Mom bazan iya rabuwa da Zainab ba ,Momy kiyi hkr itama ki bata haƙuri pls". Bazan lamunta komai daga gareka ba. Abu ɗaya zan yarda na kuma lamun ta shine Ka bata takardar ta ,tun da ba Son ta kake ba , ka Aureta ne don wani manufa taka ta dabam...Saboda taurarriyar zuciyar ka , Yau duk ya ƙare kaji ai?".  Ta ƙare maganan tana wurga masa littafin gaban ta da biro . Sallaman Adda Raliya ne ya katse masu abun da sukeyi , Wannan yasa Habab kallon inda Hjy Raliya take tana takowa cikin takon ta na manya mata . Zama tayi gyefen Inda Habab ke zaune tana dafa shi , idonun sa ya ɗago yana kallon ta kana yace " Adda Raliya kiba Momy haƙuri ta bani Matata!

Ware ido Zainabu tayi tana mmkin ashe ba ita bane kaɗai yake mawa rashin kunyar ,duk da wannan kaɗan ne akan wanda yake mata don ita harda ma tsantsan rainin hankali. In banda rainin hankali a gaban sune yake ce mata wai Abashi matar shi?". Murmushi Adda Raliya tayi tana shafa kansa kana ta juya da kallon ta zuwa ga Momy da ta haɗe rai , Zainabu tana bin shi da kallon wallh baka isa ba".  Momy kiyi haƙuri akan dukkan abun da ya faru mu ɗauke shi matsayin mu jarabbi ƙaddara bata wuce kan kowa". Kuma Momy mun zo biko ne muna sake roƙon ki akan ki dawo gidan Daddy da zama , ki cigaba da kulawa da mu kaman da baya".

Haɗa ido su duka sukayi suna kallon juna , kana Habab ya miƙe yana ba Zainabu takardar da

bata san na meye ,wani irin bugawa taji ƙirjin ta yayi da ƙarfi ,amma sai ta dake tana kai hannun ta tana amsa.....juyawa yayi yana nufar ƙaramar falon Momy ,wanda su duka suka tsaya bin sa da kallon me yake nufi???

Ma'aikatan gidan ne suka ga suna shigo maasa da kayan sa ,wanda cikin sauri Momy tace wannan kayan kuma fah na waye??? . Ɗaya daga cikin su ne yace " na Soja ne ya dawo da zaman sa nan gidan ,yace a yi masa gyara yanxu!!!!

Eiyeeeee!!!!! Zainabu tayi mgnn tana kama kwankwaso ,wannan wani irin rainin hankali ne da wayo ????????

Mmn teddy🧸
[7/1, 11:36] my number: *🕊️ƘWRTN MANYA🕊️*

_*Mmn teddy*_
34

*Littafin na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932*

****

Murmushi Adda Raliya keyi cike da jin daɗin yanke shawarar da Habab yayi ,kinga dole idan suka ganshi a cikin gidan ya nasu sukuni ,Momy zata bashi matar sa ,kuma itama zata koma gidan mijin ta.  To ina zai zauna anan? Taɓ Momy zama da wai xaiyi anan gidan?? Zainabu tace tana kallon Mom Salma da ta tsaya tunanin ya zata ɓullo mawa lamarin Habab". Jin shirun nata yasa Adda Raliya amsan takardan da yaba Zainabu ,tana buɗewa murmushi suka ga tanayi kamin ta sa dariya tana cewa " ZeeHabab kenan! Wani irin dammm yaji ƙirjin ta ya buga ,wanda yasa Zainabu saurin shigewa falon tana nufar inda Habab ya shiga".  Tsaye ta taddashi jikin window ɗin  falon ,idon sa na akan ƴan tsirarun ma'aikatan dake ƙular mawa Mom Salma da gidan nata.... Tsayawa tayi bayan sa tana bin sa da wani kallo , haushi n sa takeji na mamaye ta ,musamman tuno da kala kalan ixiyan da yayi ta mata , hannun ta ta kalla da yanxu bakace da karaya a hannun ba , sai shafa gyefen fuskar ta da tayi tana tuno da marin da tasha marar adadi a hannun shi....ɗan tsaki tajah mai sauti , wanda kamin yayi magana yaji muryar ta tana cewa" Malam mai kuma kazo yi mana anan? Gaskiya ka koma inda ka fito ,don bana ƙaunar

buɗe idanuwan na ga fuskar ka ,bana Son ka bana Son ganin ka Habab". Tayi maganan tana zubda hawaye dake sakko mata. Duk maganan da take masa ko motsawa baiyi ba , sai ma haɗe hannayen sa da yayi wuri biyu". Ganin yana shirin maida ta zauwatacciyya yasa ta ƙara matsawa garesa tana cewa " kaji mai dai nace maka ko?? , To ka sakennn.....Juyowa yayi yana bin ta da wani irin kallo da yasa ta yin shiru sai bin sa da harara take yi .... Me kike cewa ? Na rabu dake ,bakya sona ?? To Naji ,amma Ni ba zan rabu dake ba Zainab , Saboda ina Sonki , idan kuma kika matsa zaki rabu dani , wallahi da ƙafar ki sai kin dawo ,saboda Ni ɗin nan da kika ganni mugu ne ,xanyi maku mugun tan da dole ki dawo gareni ,idan kuma kika sa kafiya kika ƙi to sai dai mu ƙare rayuwar mu a haka ,ke ba miji Ni ba mata. Sakin baki Zainabu tayi tana kallon sa da mamakin ƙiƙirarin da yake mawa kansa na shi mugu ne , zai yi mata mugun tan kenan?? Na shiga uku ,abun da Zainabu ke faɗi kenan tana bin sa da kallo da cigaba da sauraren sa. Ki zaɓi ɗaya ko rabuwa dani ko cigaba da zama dani?....yayi maganan fuskar sa ba wasa a ciki? Yana matsowa dab da ita". Haɗe rai Zainabu tayi kaman bata tsorata da maganganun sa ba tace " Mai ya kawo ka ? Ka fice Habab don Allah ka bani... Ji tayi ya rungume ta yana haɗe bakin shi da nata mutsu² take tana Son ƙwatar kan ta ,amma ina sam ta kasa sakamakon wani riƙo da yayi mata... Mom Salma ce ta shigo don itama tayi masa nata faɗan ,nan taga ya riƙe Zainabu da take son ƙwatar kanta ,amma ta kasa". Kirar Sunan sa Tayi da ƙarfi " Habab! Wanda anan ne ya tsagaita badon ya soba yana cika ta daga jikin shi . Saurin baya Zainabu tayi tana goge ƙwallahn da ya taru mata tana cuno baki gaba da cewa " Wallahi Allah ya isa! Dariya taga yasa mata sam bai damu da ganin Mom Salma ba da itama ta tsaya tana ganin rashin kunya irin na Habab . Kice mawa Mom ta tabani ke,idan ba haka ba kene da kunya , don inaaaa.... Nufo sa Mom tayi nan yayi baya da sauri yana tsagaitawa da maganan tasa yana dariya".

Habab fice mun daga gida! Mom tayi maganan fuskar ta ba wasa . Murmushi yake yana cewa " To ai Mom Ni ɗan ki ne , kuma nan gidan Momy na ne anan zan kwana". Ehhhh ka kwana a ina? Allah shi kyauta ,ka hanani sukuni da Zainab kenan fita!!

Murmushi yayi yana tuno da inama momy ta barshi ya kwana a gidan da tabbas cikin dare sai ya turmushe Zeee don ya gaji da haƙuri ,ƙwartancin dai ya daina yi ,tun da ya samu Zee ya kuma ɗan ɗani zuman ta". Momy na tuba don Allah ki barni na zauna ,zan ƙoƙari na kauda kai na akan Zainab indai wannan ne tunanin ki . Kai baka isa ba ,ai ka girma nemi gidan ka ,nan gida na ne nida Bby na".

Tom Momy ki tambayi Zainab inda bata So na ,ta faɗa maki sai in tafi . Ban gane ba? Mom Salma tayi maganan tana kallon shi ,itako Zainabu sunkuyar da kanta tayi ƙasa tana wasa da ƴan yatsun hannunta. Ehh Momy ki bari ki tambayi Zainab in tace " Bata so na sai ki rabamu in kuma tace tana Sona to sai ki barni na zauna anan tare da Matata".

Humm numfasawa Mom tayi tana cewa Ok shikenan". Zainab kina Son Habab ? . Kirjin Zainabu

ne ya buga , shiru tayi tana sauke kanta ƙasa ta kasa ce mawa Momy komai". Kar kiji nauyi na Zainab , kar kuma ya baki tsoro faɗa mun kina Son komawa gidan shi??? Ƙasa bata amsa tayi sai hawaye n da ya fara zuba mata. Shikam Habab Murmushi yake don yasan ya riga ya gama tsorata Zainabu da maganganun burgar da yagama yi mata , wanda a yanda yake jin kansa yake zai iya aikata komai akan duk wanda yayi yunƙurin Rabashi da Zainabu. Zainab baki ce komai ba?? Yaji Muryar Momy yana katse ta. Dariya yasa yana cewa " Mom tana jin kunyar ki ne bazata yi maki magana ba ,amma ina mahaukacin Son Zee itama kuma haka take So n Habab.

Shiru Momy tayi sai kawai ta saki murmushi tana rungume Habab shima Rungume ta yayi , fuskar su su duka na fidda Annuri ....hannu takai tana matso da Zainabu da tayi shiru har lokacin kanta na a ƙasa , haɗa su tayi su duka tana Rungume su tana tsakiyar su.... murmushi Zainabu tayi tana ƙara riƙe hannun Momy. Ɗago da fuskar ta tayi ,nan taga idon Habab na akan ta , kashe mata 1 eye yayi wanda yasa ta saurin ƙasa danata idon". Momy ne ta goge ƙwallahn dake zubowa daga idon ta , tana ƙara godiya ma Allah". Ganin haka yasa Habab kai hannun sa yana sa hankie yana goge mata hawayen....kallon sa tayi tana murmushi ,nan suka ƙara Rungume junan su...tana riƙe da hannun Zainabu dake bin su da murmushi sosai suka burgeta , A wannan yanayin Adda Raliya ta shigo ta tadda su... Kissing ɗin Momyn nasa yayi yana Rarrashin ta... Murmushi Momy tayi tana waigawa ga Adda Raliya kana tace " Na amince Zainab zata koma ,amma ba ayau ba ,shi kuma ya koma ba bu wurin kwanan sa anan!

Rintse ido Habab yayi don ya fahimci Momy ta gane shi sosai tasan akwai abun da yake nufi. Dariya Adda Raliya tasa tana cewa " Ai ko a hakan muna godiya'.

A tare suka nufi falo ,ban da Zainabu da tayi bedroom ɗin ta ,ji tayi duk jikin ta yayi mata sanyi , gaba ɗaya Habab ya sauya , tabbas ba yaudara a tare dashi duk abun da ya faɗa xaiyi hakan ne har a zuciyar shi..............zama tayi a gyefen ƙayataccen bed ɗin nata tana sa hannun tana....

*Littafin ƙwrtn mny na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932 "Tncuuu".🤝🏻*

Mmn teddy🧸
[7/3, 15:58] Matar Doctor: *Littafin na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932*

Tana gyara Fillon dake bayan ta ...lumshe ido tayi tana tunanin abubuwa da yawa da suka faru tun daga farkon haɗuwar ta da Habab da yanda ta sharara masa mari a mall wai taje siyayya da kuɗin hannun ta da basu kai sun komo ba... Dariya ta keche dashi tana girgiza kai kurum. Ɓangaren Safiya kuwa tun da wannan abun ya faru labari yayi tangwarma har gida jen Auren su ,yanda kowa labarin da yake bada wa akan su daban....Masu cewa sun haɗu zasu kashe mahaifin su saboda son abun duniya su suka fi yawa. Wanda jin hakan yasa a lokaci ɗaya mazajen nasu suka basu takardan sakin su da cewa " Suma da suke zaune dasu ba don Allah bane , Suna samun wata dama zasu idda nufin su akan su. A kwana uku Hjy Luba da mabiyan ta sun rasa inda zasu saka kansu ,duniya tayi masu faɗi matuƙa ,kullum a cikin zullumi da fargaba suke , ga baƙin cikin tijarar da Mahaifiyar Sobreen tayi masu , don koda suka je gidan ta da sunan ta basu mafaka , sai korar cin mutunci tayi masu kaman bata taɓa sanin ɗayan su ko su duka a rayuwa ba . Cewa ma tayi a subar mata gida tana lallaɓa auren ta kar su zo su kashe mata , hummm tabbas Hajiya Luba a lokacin tasan meye rayuwa ? Musamman idan kana dashi ka dawo babu! , Shema'u ce mai'aikaciyar asibitin gomnati under federal wannan yasa ta sama masu gida a cikin Staff couters . Don babu ɗayan su da ya mallaka gida na kansa, a tunanin su kawai Alhaji Ahmadu na mutuwa zasu danni arxiƙi ,gida jen sa da koman sa nasu ne. Sai dai yanxu duniya ta juya masu...wannan yasa a ɗan kwanakin nan har rama sukayi na wahala da tashin hankali. Ana haka a satin aka kori Shema'u daga aikin nata , wanda wannan yasa Hajiya Luba har suma tayi nan take gauuuuu....a dai asibiti ta farfaɗo tana kukan nadama da baƙin ciki na rasa inda zasu nufa kuma!

******

Bayan Mom Salma ta amince da komawar Zainabu ga Habab ne , kwatsam a wannan dare akayo ƙirar su daga Lagos zuwa KD duba ga wasu miyagun da suka fara addaban mutanen Nigeria , wannan yasa akayi masu kirar gaggawa don ɓadda wannan ɓarakan". Da subahi bayan fitowar sa masallaci yake sanar mawa Daddy , haɗi da sanar masa da tafiyar tasa kamin gari yayi haske , duk da jirgi zai bi zuwa Kaduna". Nan Daddy sosai yayi masa Addu'a Allah ya kaishi lafiya ya cimma abun da ya tafi nema". Gari bai gama Haske ba ya nufi Gidan Mom Salma da fitowan ta kenan falo daga bedroom ta ganshi zaune cikin shigar sa ta kaki , komai nasa a ready yake ,alamun tafiya ". Wani sanyi taji a ƙirjin ta ganin sa cikin shigar da tafi So tun yana yaro take da burin ganin shi a hakan ,kuma gashi yanzu Allah ya cika mata burin ta .. ɓangare ɗaya ne na kuma zuciyar ta ke mata fargaba da tambayan ina Habab zai tafi da wannan sanyin safiyan??". Sojana kai ne da wannan safiyar lafiya dai ko? Ko kazo ɗaukar Zee ne ,don Nasan ka da naci da axuza. Murmushi Habab yayi yana gaishe da Mom da mata bark da safy , kana yake sanar mata da tafiyar da ta taso masa ta gaggawa". Tsammmm Momy tayi kana tace " To Allah ya dawo dakai lafy Habab ,kaje ka duba matan naka , ina tunanin ta koma bacci gaskiya ,amma kaje ka duba ta". Murmushi yayi mawa Momy kana ya miƙe don ganin Zainabu n da dama hakan yake buƙata". Koda ya shiga bedroom ɗin ta can tsakiyar gadon ya hangota ta rufa da bargo da alamun tana jin daɗin baccin a wannan lokacin. Karasawa yayi yana takawa zuwa inda take kwance yana sa gwiwowin sa ƙasa. Hannun ta ya riƙe a hankali yana matsa mata su ,ko zata buɗe idanun ta ,amma sai ajiyar zuciya ta sauke tana ƙara sauke numfashi a hankali , murmushi yayi don ya lura baccin yayi mata nisa sosai...wannan yasa shi kai bakin shi yana kissing ɗin saman goshin ta , yana shafa fuskar ta ....kusan minti goma yana a haka kamin ya miƙe da ga tsaye yana gyara mata abun rufa yana fitowa falon Momy don bai

son tashin Zainabu n a yanda take jin daɗin baccin nata". Momy taso ya tsaya yayi breakfast amma sai yace " Lokaci zai ƙure masa ,wannan yasa ta bin sa har wurin da yy parking tana masa addu'oi ,kana ya fice daga gidan cike da farin cikin ganin yanda Komai na rayuwar sa ya koma masa tamkar da baya cike da jin daɗi ya nufi airport. Ita ko Momy har ya fice ta kasa komawa ,kawai sai jin ƙwallah tayi na bin kuncin ta , kewan Habab da tausayin sa suka rufe ta , falon ta juya tana komawa , don haɗa masu break fast ,tasan jiya Zainabu kwana tayi tana zazzaɓi ,sai da ta taimaka mata da magunguna sannan taji dai dai , wannan yasata koda ta farka da asuba tana sallah ta koma baccin ta....haka dai Momy tayi ta aikin ta ,tana murmushi haɗi da cewa a zuciyar ta" Allah yasa abun da nake hasashe ya zama gaskiya".
*****
Tafiya sukeyi idon su rufe basa ko ganin gaban su...kashe mun ke zaiyi?? Ina bazai yiwu ba ,ga tukwicin saki ga kuma shi yana shirin kashe mun ke Sobreen?? Tabbas sai na kaisa kotu ,kotun ƙoliii kuwa, muje sobreen ,nemo mana keke mu hau yanxu zamu tafi kotun ƙoli....Ammin Sobreen ke tafe tana sambatu na mahaukata , wanda nesa na hango Sobreen tana gudu haɗi da ƙwala kirar sunan ta Ummma!! Amma ina gaba tayi tana shiga titi wannan abun hawa ya kauce mata ,wancenn ya kauce mata". Isowan Sobreen yasata saurin jan hannun ta tana kauda ita daga titin ,kana tace " Umma sati nawa da barin mu gidan Abba , muyi hakuri komai ya faru damu mu muka jah mawa kanmu". Tayi maganan tana goge hawayen fuskar ta , da tayi baƙi wannan farin fatan da ake ƙafulle dashi ya jeme ta lalace tamkar ba ita ba. Sobreen!! Taji an kirata cike da mmki ta juya ganin su Shema'u da Hjy Luba suma a wulaƙance ". Kunya ne ya kama Sobreen wanda yasata kasa haɗa ido da su sai sunkuyar da kanta ƙasa tayi tana cigaba da zuban hawaye". Mai ya sameta ??? Hjy Luba tayi maganan tana nufar inda Mahaifiyar Sobreen take ta duƙa tana ta tsintar ledoji . Cike da Muryar kuka Sobreen take basu labarin sakin da mahaifin ta yayi mawa Umman nata , da kuma dukan da yayi mata tamkar zai kashe ta ....wanda ruɗun rabuwar su yasata haukacewa...... Salati Hjy Luba tasa tana rushewa da kuka , wanda suna tsaka da hakan ne Suka ga Umman Sobreen ta razana tana jah baya da cewa " Ni ne Alh nafi'u zai saki?? Bazai yiwu ba sai na kai sa kotun ƙoli tana maganan haɗi da fallawa da gudu tana nufar titi , bin ta sukayi suna cewa " Taimako a kamata a riƙe , amma ina tuni ta shige ma titin , wani babban moto ne yayo kan babban titin ,wanda jah baya su Hjy Luba sukayi suna sakin wani gigitaccen ihu ganin moton yabi takan Umman Sobreen.... Sobreen kuwa ganin hakan yasata zubewa wurin gwiwowin ta ƙasa tana tsaga ihu.... Mutane ne suka rufe wurin ciki harda Alh nafi'u mahaifin ta da dama yake neman ta ta bashi ƴar sa . Da ita kenan masa wato Sobreen ya ɗauki alƙawarin aura mawa koma waye koda kuturu ne".
[7/3, 16:01] Matar Doctor: *Littafin na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne  MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932*

****
[7/3, 16:44] Matar Doctor: *Littafin na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne  MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932*

Mutane kuwa daga masu kama kai sai masu ihu ganin irin daga dagan da Umman Sobreen tayi

ta haɗe da kwalta , inalillahi wa'inna ilaihir raji'un shine kaɗai abun da Hjy Luba ke cewa " ruɗu iya ruɗu tashi ga a wannan rana .. Alh Nafi'u ne ya kama hannun Sobreen da take ihu kaman ranta zai fita ,yana jefa ta a moto yana jahh haɗi da barin wurin , don ko a jikin sa ganin wannan haɗari , cewa ma yake hakkin mahaifiyar sa ne , da ta raɓasu tsawon shekaru. Don haka can zai kai Sobreen garin Adamawa ta koya mata tarbiya kaman sauran ƴaƴan da ya saba gani. Zainabu kuwa sam bata farka ba sai wuraren 9:00am ,wanda da addu'a a bakin ta ta miƙe , tana kirar sunan Habab , sai da idon ta yaƙara buɗe wa ne ta tabbatar da mafarki tayi". Dafe ƙirjin ta tayi da yake harba mata da ƙarfi tana cewa " Meke shirin faruwa da Habab ?? Allah kasa mafarki ne ba gaskiya bane . Kasa nufar toilet tayi sai kawai nufan falon tayi don ganin Momy a wani hali take ciki don tasan jiya a kanta ta kwana". Cike da murmushi Momy take bin Zainabu da kallo da tayi wani dama² tayi kyau ta murje sai ƙiban ta take mai sukuni da natsuwa. Cike da harka Zainabu ta ke yin mata an tashi Ify? Kana ta nufi kitchen don taimaka mata aiki. A'a Zainab koma kije ki huta , na kammala komai ai , yanxu ke nake jira ki shirya kizo kiyi breakfast sai kisha maganin ki". Nisawa Zainabu tayi tana murmushi da mata sannu da aiki ,kana ta juya don ta watsa Ruwa ta sauya kayan jikin ta daga na barcin zuwa na zaman gida". Cike da jin ƙaunar Zainabu n Mom Salma kebin ta da kallo , tabbas abun da take hasashe hakan yake , juna biyun jikin ta na nan bai fita ba ,Allah kenan! Allah ya raba lafiya". Mom Salma tayi maganan tana cigaba da shirya dirnng area n. Motsin Zainabu ne yasata ce mata " Bismillah zauna dai da lura! To Momy". Zainabu tayi maganan tana zama a hankali duk jikin ta nauyin shi take ji a kwana biyu sai tana rinƙa jin ba daɗi a harshen ta ,kome xata ci bata jin daɗin shi....nan tafara break cike da gode mawa Mom Salma don iya girki da karamci ba baya ba". Gaskiya Mom Komai yayi daɗi". Zainabu tayi magana tana dariya. Dariya itama Momy tayi tana cewa " mashaallh to tun da Zee ta yaba saura ɗan ƙaƙƙwafi Habab! Ohhh!! Ɗazu fa Habab yazo gidan nan kina bacci tfy aiki ya kamasa a yau ɗin nan yanxu ma ina tunanin jirgin su ya ɗaga gasky". Wani irin bugawa ƙirjin Zainabu yayi , wanda sakin cup ɗin tea tayi tana cewa " Momy meyasa kika bar sa ya tafi?? Wallh tsoro nakeji nayi mafarki Momy ki kirasa ya dawo!!!. Ganin Zainabu ta ruɗe lokaci ɗaya yasa Mom Salma saurin dafata tana ɗan bubbaga kafaɗan ta da cewa " Shiiii... Ya isa ai zai dawo yace baifi 1 mount zaiyi ba , kuma mafarki Zainab ba gaskiya bane ba kinji ,Allah zai dawo maki da Habab lafiya inshaallh". Nisawa Zainabu tayi ji tayi komai ya fice mata a rai. A hankali ta ce " To Momy Allah yasa". Amin abun da Mom Salma tace kenan tana cigaba da matsar mata da irish gaban ta.

****

Kwana uku da tafiyar Habab Daddy da Kanshi yazo bikon Mom Salma ,wanda iyaye sun shiga cikin maganan sosai da ƴan uwa da suke ta zuruntu garuruwa kuwa ,wannan yasa don dole Mom Salma ta kuma amincewa , a satin a ka maida auren su da Daddy ,duk da ba wani taro akayi ba,manya ne a dangi suka taru...a kuma ranan Mom Salma da Zainabu da baki yaƙi rufuwa saboda farin ciki suka koma gidan Daddy. Da komai na gidan sai da aka sake , niko nace sabon gwamnati kenan shi aka kafa". A ɓangaren Zainabu ke zaune ,kula da gata iri iri take gani a wurin Momy da Daddy kowann su na ƙoƙarin ganin sun faran ta mata ,sun kawar mata da dukkan wani damuwa . Wanda a yanxu kusan wata ɗaya kenan da tafiyar Habab . A yau ne Zainabu ta shirya don zuwa gidan Umman ta ,wanda a yanxu idan kaga Zainabu komai na alamun masu ɗauke da juna biyu ya bayyana mata , gashi bai fara girma ba ,amma ya sata tayi kyau matuƙa ,duk da da hutu da kula irin na Mom Salma da take bata".

Farin ciki da taje gidan ba'a magana wurin mutan gidan da su Abba ,bana har da Sama'ila anan nan da ita ,wanda sosai taji daɗin hakan , Zainabu fah anyi hankali don har da tsaraba takai mawa su Umma da sauran yaran gida. Anan take jin ashe Habab sai da yazo sukayi sallama sannan ya wuce. Wurare n yammaci ta tattara tana komawa gidan Daddy. A falo ne take jin kukan mutane da magiya na ban haƙuri ,wanda yasata kutsa kanta cikin sauri , idon ta ne ya sauka akan Hjy Luba da Shema safiya dukan su a falon gaban daddyy ,gyefe guda kuma Mom Salma ce itama fuskar ta ɗauke da damuwa.........

*Littafin na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932*
[7/4, 16:55] Matar Doctor: *Littafin na kuɗi ne Don Allah kar ki karanta indai baki biya ba, normal group ₦300 Vip group₦500 Spc ₦1000 via 👉 6037312299 Mohammed Aisha keystone bank ,idan kuma kati ne MTN zaku Turo ta wannan number 08081202932*

Jiki a sanyaye Zainabu ta isa tsakiyar falon tana zama gyefen Adda Raliya da itama ke share ƙwallah ganin yanda Uwar tasu duk ta mozan ta ,duk da da halin ta amma kuma uwa uwace ! Zama Zainabu tayi a ƙasa a hankali tana jin yanda Safiya da Shema'u keba ma Alh Ahmadu Haƙuri harda Hjy Luba , wanda cike da Muryar girma Alh Ahmadu ke cewa " Ya yafe masu Allah shi yafe mana baki ɗaya". Jin hakan yasa Su Hjy Luba juyowa ga Momy da Zainabu da kanta ke a ƙasa suna bata haƙuri akan abubuwan da suka ai ƙata da yanda ta kori Momy da hannun ta duk don kishi da masifa". Cike da nuna komai ya wuce suka ce Allah ya yafema na baki ɗaya". Wani irin Zainabu taji ganin wai Hjy Luba ce take yi masu sallama zata bar gidan ita da su Safiya. , Wanda ganin hakan yasa Momy kallon Daddy tana cewa " Ya kuma zaka barsu su tafi? Don Allah dai kayi haƙuri akan komai mu ɗauke shi muƙaddari dama rubuta ce ne Allah ya tsara xaya faru.  Maganganun Momy ne yayi tasiri a zuciyar Daddy , wanda sai da suka fita ne yake ce mawa Adda Raliya ta kai su ɗaya daga cikin gidajen sa na High low cost , ya bama Hjy Luba har muddan rai , su Safiya su zauna can , har Allah ya basu bazajen aure ,idan kuma auren nasu ya dai daita Alhmdullh". Ba Adda Raliya ce kaɗai tayi godiya ba , har da Zainabu da farin ciki yaki ɓoyiwu a fuskar ta , don ganin Hjy Luba a wannan hali ba ƙaramin ɗaga mata hankali yayi ba". Godiya sukayi ta mawa Daddy har ya shige side ɗin shi ,kana Adda Raliya ta fice da sauri don sanar mawa su Hjy Luba da kyautar da karamcin da  Daddy yayi mata... Momy ne ta kalli Zainabu tana murmushi kana tace " Har kin dawo yasu umma?? Suna lafiya Momy sunce a gaishe ki". Cike da jin daɗi Mom Salma tace " to mashaallh ina gdy. Tun daga nan shiru ne ya biyo bayan su tsawon lokaci ,kamin Zainabu ta katse shirun da cewa " Momy wai don Allah nayi maki wata tambaya ,Allah yasa bazai ɓata maki ba , don a kan rayuwar ki ne Momy da na Habab!

Murmushi Mom Salma tayi kana tace " Haba ɗiyata faɗi maganan ki mana ? . Gyara zama Zainabu tayi tana kama hannayen ta kaman mai shirin bada labarin wani abu ,kana tace " Har yau Habab bai san daliln barinki gidan Daddy ba , anai meki an rasa , kin rabu dashi da Daddy ,wanda ada baya akan su ki rabu da komai naki ƴan uwa ƙasar ki da kowa naki ,amma Momy

